NAZARI A KAN KIRARIN ABINCIN HAUSAWA

DAGA

AHMED ALIYU Ph.D

aliyuahmed779@gmail.com

08065402292

DA

SALIHU ILIYASU SULLUBAWA Ph.D

salihusullibawa@gmail.com

08065278653

SASHEN KOYAR DA HAUSA NA KWALEJIN ILIMI DA KOYON SHARI'A TA YUSUFU BALA USMAN, DA KE DAURA. JIHAR KATSINA.

SATUMBA, 2026

Tsakure

A cikin kowace al'umma abinci da tufafi da muhalli na daga cikin abin tinqaho da su, al'ummar

Hausawa mutane ne masu riqo da al'adunsu na gargajiya, musamman wajen waxanda suke gudanarwa a rayuwarsu ta yau da kullum. Hanyar da aka bi wajen gudanar da wannan bincike sun haxa da, tattaunawa da mutane da karantowa daga rubutattun

bayanai. Qudirin wannan takarda shi ne ya binciko tare da tattaro bayanai a kan kirarin abinci na Hausawa tare da tattaunawa ko rarrabe tsakanin aya da tsakuwa, ganin yadda yawanci abinci gargajiya ke neman zama tarihi a idanuwan Hausawa sakamakon cuxanya da wasu al'ummomi na kusa da na nesa, kamar Larabawa da Turawa da Fulani da Buzaye da Nufawa da kuma Yarabawa da sauransu. Daga qarshe, an gano cewa akwai kirari cunkushe a cikin abincin Hausawa na gargajiya da zaka tarar suna yi domin havaka harshe da kuma raya al'adun Hausawa.

1.0 Gabatarwa

Kirari na xaya daga cikin vangaren maganganun hikima wanda al'ummar Hausawa ke gudanarwa a zamantakewar rayuwarsu ta yau da kullum. Wannan takardar ta yi magana a kan kirarin abincin Hausawa wanda suke ci a tsakaninsu domin kawar da yunwa da kuma sama ma jikinsu lafiya. Da farko an kawo ma'anar al'ada da kirari da ta abinci da ire-iren abubuwan da ake ma kirari wanda ya haxa da na mutane da garuwa da na dabbobi da sauran abubuwan da suka danganci rayuwa ta yau da kullum wanda abinci yana xaya da daga cikin manya manyan cikin su da sutura da suransu, daga nan aka kawo kaxan daga cikin ire-iren abincin Hausawa da kirarinsu.

1.1 Ma'anar Al'ada

Al'ada na a matsayin dukkan rayuwar xan'Adam tun daga haihuwa har zuwa mutuwarsa, matakan rayuwar kuwa su ne aure da haihuwa da mutuwa, kuma su ne ginshiqin ginin al'adunsa, (Bunza, 2006: xxi).

Domin al'ummar Hausawa ba suna zaune haka nan kara zube ba, watau ba kai ba

gindi, suna da tsararriyar al‘ada wadda ta shafi yadda suke tafiyar da rayuwarsu ta yau da kullum. A gaskiya ma ko da addinin musulunci ya shigo qasar Hausa ya tarar da Hausawa na tafiyar da harkokin rayuwarsu bisa ingantaccen tsarin da ya shafi yadda ake tafiyar da harkokin aure da haihuwa da mutuwa da sauran ma‘amalolin rayuwa, (Sallau, 2010:5).

1.2 Bitar Ayyuka Masu Alaqa da Wannan Aiki

Rimmer da wasu (1966) a cikin littafinsu mai suna Zaman Mutum da Sana’arsa, sun lissafo sana‘o‘in Hausawa na gargajiya irin su noma da qira tare da kirarin kowace sana‘a. Wannan littafi ya qara ba mu haske wajen fahimtar wannan bincike da muke a kan kirarin abinci na Hausawa.

Garba (1991), a wani littafi mai suna Sana’o’in Gargajiya na Hausawa a cikin littafin ya lissafo sana‘o‘in Hausawa na gargajiya irinsu, noma da kiwo da qira da suke tare da kirarinsu.

Don haka, wannan littafi ya taimaka mana qwarai da gaske a vangaren kirarin sana‘o‘in Hausawa.

Alhassan da wasu (1982) cikin littafinsa mai suna Zaman Hausawa, ya yi magana a kan al‘adun Hausawa na gargajiya, inda ya lissafo abincin Hausawa na gargajiya irinsu gero da dawa da wake da gyaxa da masara da shinkafa da kuma kayan masarufi irinsu abarba da lemu da gwanda da kuma ayaba. Wannan littafi yana da alaqa da bincikenmu domin ya kawo nau‘o‘in abincin Hausawa na gargajiya na abinci da na marmari, wanda dukkansu sun kasance xaya daga cikin abubuwan da wannan bincike zai magana a kansu.

Haka nan, Xangambo (1984) ya bayyana kirari a matsayin yabo da zuga, kuma cikinsa ne ake amfani da sarrafa harshe cikin hikima, haka kuma kirari ka iya zama yabon kai, kamar yadda _yan tauri ko _yan dambe ke yi. Wannan aiki na Xangambo, yana da alaqa da bincikenmu.

Muhammad (2020), ya kawo ma‘anar kirari tare da zayyano kirarin da ake yiwa wasu mutane irinsu: Sarakuna da _yandambe da maqera. Saboda haka, da gani babu tambaya wannan littafi na da alaqa da binciken da muke gudanarwa musamman duka sun yi tarayya a wajen kirari.

Kirari wata sarrafaffiyar magana ce wadda a kan yi da baki domin kambama ko kururuta wata halitta ko wani abu. A nan, za a iya yiwa wani kirari ko mutum ya yi wa kansa,

(Muhammad, 2003)

Sa‘id da wasu (2006) sun ce, ―Kalmar kirari ana iya fassara ta da kalma ce ko kalmomi ne da a kan faxe su da wani salo na musamman don kambamawa da zuga ko girmama wani mutum ko wani abu.

1.2 Ma’anar Abinci

Masana da dama sun ba da ma‘anar abinci ta yadda suka fahimce shi misali, abinci na nufin duk wasu abubuwa masu qarfi da ake sawa a cikin baki wanda zai ciyar da mai rai tare da sa shi girma, (Gusau, 2012).

Wani ra‘ayin cewa ya yi abinci na nufin duk abubuwa masu qarfi waxanda ake ci da sha domin samar da kuzari da qara girma ga mutum, (Sa‘id, da wasu 2006).

A namu hangen muna ganin cewa abinci na nufin duk wani abu cimaka wanda idan mutum ko dabba suka ci shi zai yi musu maganin yunwa ya kuma gamsar da su.

Saboda haka, abincin Hausawa na nufin duk wani nau‘in abinci wanda ya shafi ganye da _ya‘yan itatuwa da tsaba da saiwa da dai sauransu waxanda Hausawa aka sani da su, kuma suke ci suke sha wanda suka gada iyaye da kakanni kuma shi ne da zarar sun ci shi ko sun sha, zai yi masu maganin yunwa ko kuma ya gamsar da su.

1.3 Nau’o’in Abinci

Ana iya rarraba nau‘in abincin Hausawa kamar nau‘in abinci na ci da na sha da na marmari da kuma na qwalama. Ta fuskar amfaninsu ga jikin xan Adam kuwa, ana iya kallon abinci kamar haka-

1. Abinci mai kuzari da qara qarfin jiki
2. Nau‘in abinci mai gina jiki
3. Abinci mai qara garkuwar jiki

4. Abinci mai sa qarfi da ruwan jiki da suransu.

1.4 Ma’anar Azancin Magana

Masana da dama sun yi qoqarin fito da ma‘anar azancin magana ta yadda suka fahimce shi misali:-

Azancin magana na nufin magana ce _yar gajera da a kan tsara cikin azanci da nuna balagar zance da ke zuwa jima-jima, (Yahaya, 1990).

Umar, (2003) ya bayyana azancin magana da nufin wata tsararriyar magana ce ta hikima da fasaha da masu hikima ke tsarawa don nuna isa da qwarewa da kuma nuna balagar harshe da ke zuwa gava-gava ko jimla-jimla ko gunguwa-gunduwa domin isar da saqo na musamman.

A wannan bincike kuwa, an yi kirdadon ma‘anar da cewa, azancin magana na nufin _yan guntattaki magana ne ko zantuka da ke gava-gava ko gunduwa-gunduwa domin isar da saqo na musamman, kuma ana tsara su da ka, a kuma isar da shi da ka kuma adana shi da ka.

Azancin magana na da rassa waxanda suka haxa da kirari da zaurance da karin magana da zambo da habaici da kaci-kaci da salon magana da ba‘a da baqar magana da sauransu.

1.5 Ma’anar Kirari

Masana da dama sun bayar da gudumuwarsu wajen kawo ma‘anoni daban-daban na kirari, daga cikin waxannan ma‘anoni da masana suka bayar sun haxa da-

Dangambo (1984) ya bayyana cewa, kirari ya qunshi yabo ko zuga ne cikin irin wannan yabon da zuga ne ake amfani da sarrafa harshe cikin hikima, kuma kirari na iya zama yabon kai kamar yadda _yan tauri ko _yan dambe ke yi.

Umar (1987), ya bayyana kirari a matsayin wata sarrafaffiyar magana ce _yar doguwa ta hikima da a kan shirya musamman don kambama mutum ko wani abu da sauran makamantansu.

Mohammad (2003) ya bayyana kirari a matsayin wata sarrafaffiyar magana ce wadda a kan yi da baki domin kambama ko kuranta wata halitta ko wani abu, a nan za a iya yiwa mutum kirari kuma zai iya yi wa kansa.

Kirari wani rukuni ne na salon sarrafa harshe da Hausawa kan yi amfani da shi wajen nuna gwanintar harshe da qimar harshe. Hausawa suna amfani da basira ta hanyar fasaha wajen yi wa dukkan abubuwa da ke cikin duniyar tamu kirari ta hanyar tsara kalmomi da suka dace da halayen abubuwan a cikin lugga mai ban sha‘awa. Idan aka yi wa abu kirari a harshen Hausa, sai kaga cewa kirarin ya dace da hali ko yanayin abun, (_Yar‘adua, 2007). Idan muka tsaya tsaf, muka dubi waxannan ma‘anoni na kirari da masana suka kawo, za mu iya bayyana kirari a matsayin magana ce ta hikima da fasaha da ake amfani da wasu kalmomi na musamman don girmamawa ko kambama wani abu ko mutum ko dabba ta fuskar halayarsa ko xabi‘unsa ko dai yadda halayarsa suke ko wani abu yake gudanarwa domin qara masa qwarin guiwa.

1.6 Ire-iren Kirari

Dangane da ire-iren kirari abu ne mai matuqar wahala a iya qayyade ire-iren kirari, saboda abu ne da ake iya kowane abu na duniya, amma duk da haka, abin da ba zai samu duka ba, ba kuma za a bar shi duka ba, kaxan daga ciki akwai-

1. Kirarin mutane
2. Sarakuna da masu mulki
3. Kirarin garuruwa
4. Akwai na dabbobi
5. Kirarin abinci
6. Akwai na sana‘o‘i, da sauransu.

1.7 Abincin Hausawa da Kirarinsu

Abincin Hausawa abinci ne wanda al‘ummar suka gada tun kaka da kakanni, wani kuma ya zo masu sakamakon cuxanya da baqi na kusa da na nesa, wato abinci ne da al‘ummar Hausawa ke ci domin ya gamsar da su kuma ya yi masu maganin yunwa. Sakamakon

muhimmancin da gare su shi yasa Hausawa suke qoqarin kambama su ta hanyar yi masu kirari, ga wasu daga cikin sunyen abincin Hausawa tare da kirarinsu kamar haka-

Sunan Abinci		Kirarin Abincin
Alkaki	-	Manyan buki, in an gan ka buki ya qare
Alala	-	Alal _yar gayu, alala _yar banza
Albasa	-	Albashe bashe yaran ganye, _yar burguma da fata goma
Algaragi	-	Algaragi da miya
Alkubus	-	Cin ka sai _yan gayu, kana ci kamar ka na cin hanta
Allagira	-	Kalallava ta yara qanana
Biredi/Buredi	-	Qanzo xan hajiya, kyautarka isa, rowarka rashin kunya, manajan ka ba ya sallar jam‘i
Vula/Tuwan-ruwa	-	Hutsin tuwo, Kuturu na ganinka ya kwana da yunwa
Dabino	-	Xan itaciya mai daraja
Dabuwa	-	Cin ki sai _yar gata, cin ki sai da babban fardo
Dambu	-	A ci dambu a sha ruwa, kashe mai zari, cin ka ba ruwa hatsari ne
Xangauda/Xangabda	-	Qato da kwat, haukan banza ya ke, ashe rigarsa guda
Dankali	-	Sha kushe, dashen maza cin mata, dankalin mai saurin gimsa, ba a cin ka saida ruwa, ana cin ka ana kushe ka
Xan-narogo	-	Xannarogo taka yaga
Xan-wake	-	Xan-wake ka fi ubanka, na kacala qanan kacala, yi kwalliya ido duk kwantsa, Xan-wake da maid a yaji, qula-qulai abin jifar yunwa

Dinkim - Dinkim da quli nama ne, dinkim da quli naman talakka

Xinya - Baqar mace, baqin ki bai hana ki yin daxi ba.

Duma - Xan duma abin shan ganye

Fanke - Barka tsomin daxi, xan tsamo-tsamo na cikin mai, maza na ci

mata na ci

Fate - Fate na langa gardamar dare, da shan ka qara shan labari, da xaukar Akunsin ka gara xaukar magana, fate kandami a sha ka

ta gefe, na langa qazami shan ka sai da dabara

Fura - Farin ciniki in ba a sayar ba a sha, ta gero mai tada kunnuwan xan tsoho

Gero - Ba ka jiran dangi xan taki, in ya so ka, kai gida kai haji, kai

mota, in ya qi ka ka sha xauri har igiya ta yi rara

Gurasa - Gashin mai haquri, hantar talaka

Gyaxa - Gyxa mai sihiri a vara a ga biyu, a murza a ga huxu, a tauna a ji garxi,

ba don kin yawa ba da sai _yan sarki

Kankana - Kin yi kyau kin yi kala

Kifi - Musulmin nama, kowa ya cika ya yi amai xan wuta ne, qarkon kifi

daga ruwa zuwa wuta

Koko - Mai kamar ka huce, shan koko buqatar rai

Qosai - Qosai gayya magajin tubani, qosai da zafi-zafi tuyar yanzu

Kuka - Maganin kukan yaro

Kunu - Kunu na mutum uku, ko tsoho ko yaro ko marar lafiya, ko kunu ya

huce kai dai tsinana bakin ka,

Kunun Kanwa - Kai ba kyau ba sai haxe fuska, na mai jego in ya yi kwantai na _yan

barka

Kunun Zaqi - Na zaqi ka fi rowan banza, kwano guda tukunya goma

Quli-quli - Na quliya autan dauxa autan daxi, a ci goma ashirin, na ragaza saurayi daga nesa

Kwaxo - Mai maganin kwaxai, kwaxo ba ka gwani

Kwakwa - Farin ciki jan baya

Makani - A ci makani a je Makka in an dawo a makance, makani qanan doya Mangwaro - Xankamaru mai jijiya ya wuce sai baxi, ya bi gari ya zagaye ya hana mata haihuwa

Nama - Cimar Zaki, nama xan uwan buzu ne, sai ana ma shi ihu

Rake - Rake giredi gangariya dagargaji, kara xan fadama ga ruwa ga zaqi, ana sha ana Allah san barka, ba ana Allah wadai ba

Rama - Ramammiya ta bakin gona aman ki sai an zaro

Rogo - Rogo amfanin qasa, wanda bai sani ba ya raina kamarka. Na rogaji garin daxi, ya ragargaje ra rushe xan bana mai garin daxi, saiwa ikon Allah, Sarkin kiri ba ka isa ba ka fasa qasa

Rummace - Na Ruma qazami, a haxa xanye da dafaffe, mai tsabta yake kwana biyu, ga marar tsabta sai ya yi wata

Shaye-shaye da Romo - Shaye-shaye da romo albishirinki tsohuwa ga aljaninki ya zo

Tafasa - Ta magaji mai kai yaro gaci

Taiba/Teva - Teva abincin gwari, alallatsa ta Bature mai sa yaro ja

Taliya - Taliya-liye uwar daxi ta malam Audu cin ki kwana da Bature

Tsire - Ba kuxi ba sai an saida

Tumu - Tumu-tumun albarka, a tuma a ci a yi Allah ya kai mu

Tuwo	-	Tuwalle mai jiki duk tsoka, arne mai wuta biyu
Waina/Masa	-	Waina banzar kowa, kowa ya je gidan buki ke yake ci, waina mai tallar ki sai ya yi wayyo! Da sakal kalacin waina
Wake	-	Wake kai mu aljanna
Wake da Shinkafa	-	Qato da lagge
Wasa-wasa	-	Cin ki sai xan gayu ko _yan gayu
Yaxiya kabari na	-	Yaxe kushewata, yaxiya yaxi gidan mu in na mutu ki yaxi
_Yaryau	-	_Yaryau kin qi zaman aure
Zogala	-	Zogala gandi samari dangi/darni, zogale gandi mazan tsaye ana ginarka ka na qara tsawo.

1.8 Muhimmancin Kirarin Abincin Hausawa

Kirarin abincin Hausawa na na taka muhimmiyar rawa a cikin al‘ummar Hausawa, daga cikin muhimmancin kirarin sun haxa-

1. Domin nuna balaga da qwarewar harshe ta fannin azancin magana.
2. Yana adana al‘adun Hausawa.
3. Domin nuna muhimmancin abinci ga rayuwar al‘umma.
4. Kirari wata kafa ce da Hausawa suke tallafa hajarsu musamman abinci don jawo hankalin mai saye.
5. Domin samar da raha da annashuwa ga mai sauraro.
6. Kirarin abincin wani wuri ne na qago da qirqiro sabbin kalmomi na hikima.
7. Kirarin abinci wata farfajiya c eta bincike ga masana harshe da adabi da kuma al‘ada.

8. Bunqasa harshen Hausa musamman vangaran hikima da qaruwar kalmomi a cikin harshen.

Kammalawa

Kamar yadda bayanai suka gabata, wannan takarda ta yi tsokaci ne a kan irin kirarin abincin Hausawa wanda suke a zamantakewarsu ta yau da kullum, takardar bayan gabatarwa an kawo ma‘anar abinci da ma‘anar azancin Magana da kirari da ire-irensa, sannan aka jero abinci Hausawa da kirarin da suke masu, sannan daga qarshe aka kawo muhimmancin kirarin abincin a cikin wannan al‘umma ta Hausawa.

Manazarta

Alhassan, H. da wasu (1988) Zaman Hausawa Bugu na Biyu. Lagos: Islamic Publication Bereau.

Bunza, A.M. (2006), Gadon Fexe Al’ada, Lagos: Tiwal Publishers.

Dangambo, A. (1984) Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa, Kano: Triump Publishers Company.

Garba, C. Y. (1991). Sana'o'in Gargajiya a Qasar Hausa. Spectrum Books Limited.

Gusau, G.U. (2012). Bukukuwan Hausawa. Ol-Faith Prints.

Janaidu, I. da Yar‘adua, T.M. (2007) Harshe da Adabin Hausa a Kammale Don Manyan Makarantun Sakandare, Ibadan: Nazareth Press Ltd.

Karofi, I.A. da Tukur, A.A. (2015) ―Abincin Hausawa na Gargajiya da Tasirinsa ga Lafiyarsa‖, Takardar da Aka Gabatar Domin Qarawa Juna Sani na Qasa da Qasa na Farko, a Abuja:
Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke Zuba.

Muhammad, M.S (2020) Bahaushiyar Al’ada. Bayero University Press.

Muhammad, Y.M. (2003) Adabin Hausa Kano: University Press.

Rimmer, E.M. da Wasu, (1966) Zaman Mutum da sana’arsa N.N.P.C. Zaria

Sa‘id, B. da Wasu (Edit) (2006). Qamusun Hausa. Ahmadu Bello University Press.

Salamatu, I. da Zainab, A. (2011) ―Nazarin Karin Magana a Cikin Littafin Iliya Dan Mai Karfi‖, Kundin Bincike da Aka Gabatar a Sashen Nazarin Hausa, Dutsinma; Kwalejin Ilmi ta Isah Kaita.

Sallau, B.A. (2010), Wanzanci Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa. Kaduna: M.A. Naji'u Professional Printers, No.3 Koya Road.

Umar, M.B. (2003) Tsarin Yaxuwar Adabin Baka na Hausa, Languages Studies Vol 1, No 1.

Yahaya, I. Y. Da Wasu (1990) Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare na 2. Ibadan: University Press.

Zaruk, R.M. da Wasu (1990) Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Makarantun Sakandare na 3, Ibadan: University Press.